# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na goma: Birgimar Hankaka

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Lami: 'yar shekara 20
Malam Talle: ɗan shekara 60
Matar M Talle: 'yar shekara 55
Magaji: ɗan shekara 22
Indo: 'yar shekara 20
Faisal: ɗan shekara 19
Jami'in tsaron kan iyakar teku: ɗan shekara 40
Ɗan fasa-ƙwauri: ɗan shekara 45

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu". Wannan shi ne kashi na goma daga cikin wasan kwaikwayonmu na wannan gidan rediyo mai taken "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". Muna duba ne a kan yin ƙaura ta halattacciya da kuma haramtacciyar hanya da 'yan Afirka ke yi zuwa wurin da suke ganin shi ne wani tudun mun tsira, wato Turai. Lami dai tana ta aiki a matsayin sabis ba da izini ba a wani gidan rawa na Turai, aikin da ƙawarta Sa'adatu ta sama mata. A can gida Afirka kuma, Magaji ya daɗe bai ji labarin Lami ba kuma har ya fara damuwa. Don haka sai ya je gidan su Lami don ya ji ko lafiya, sai dai zuwan nasa ya sa ya fahimci iyayen Lami na fama da matsalar kuɗi.

A ɗaya ɓangaren kuma mutanen namu, wato Faisal da Suleman, waɗanda ke can Arewacin Afirka sun tafka muhawara a kan ko su bar ƙasarsu wadda ke fama da rikicin siyasa.

A wannan shirin na yau mai suna "Birgimar Hankaka", wanda za mu fara daga gidan Malam Talle inda Lami ta dawo daga Turai haka kwatsam, ba zato ba tsammani. Iyayenta sun yi mamakin yadda suka ga 'yarsu ta sauya, ta zama wata iri dabam. Bari mu ji irin hirar da suke yi yayin da suke cin abincin dare.

**Fitowa ta 1: Lami tana cin abinci tare da iyayenta**

**Lami:** Kai! Sauro ya yi yawa!

**Matar M. Talle:** Abin kamar a mafarki! Yanzu ke ce a gidan nan namu, Lami!

**Malam Talle:** Ai, lokacin da na buɗe ƙofa na gan ki a tsaye da kayanki, sai na ji kamar a mafarki. Wannan shi ne abin da ya fi daɗaɗa min rai a rayuwata!

**Lami:** Don Allah Baba, in ba za ku damu ba zan rufe tagogin nan. Sauro yana shigowa.

**Matar M. Talle:** Me zai hana. Ki rufe mana! Ai gidanki ne Lami. To ci gaba da faɗa mana labarin Turai, da labarin karatu, da aiki, da kuma ƙawayenki. Gaba ɗaya kin canza Lami, wallahi!

**Malam Talle:** Wallahi kuwa, amma dai da ganin ki kina samun kuɗi sosai. Kin ga kin sa kaya da takalma masu kyau. Ga babbar waya, ga sabuwar *laptop*, ga sabon agogo, ga sabuwar…

**Matar M. Talle:** Ka ce 'sabuwar Lami' kawai! Wannan shi ya kamata ka faɗa, wata sabuwar Lami fa. To faɗa mana, wace irin sana'a kike yi da har kika iya sayen irin waɗannan kaya, Lami?

**Lami:** E to, ina yin aikatau ne. A Turai irin wannan aikin na ci sosai. Don Allah ku ɗan tsahirta min, in ba za ku damu ba ina son na ɗan fita na ga ƙawayena.

**Malam Talle:** Me zai hana. Na san za ki ga abubuwa sun sauya mana 'yan kwanakin nan, Lami. Haka muke tun da aka sallame mu daga aiki. An ma yanke mana wuta saboda ba ma iya biya. Shi ya sa muke zaune a cikin duhu.

**Lami:** Ungo, ga Yuro ɗari biyar nan. Ina jin za ta isa, ko kuwa?

**Malam Talle:** Mun gode, Lami. Allah Ya saka da alheri.

**Mai ba da labari:**

Lami sai harka take yi kamar wata mai arziki wadda ta san ya kamata kuma mai kyauta. Amma ba ta yi wa iyayenta bayanin haƙiƙanin abin da take yi ta samu irin wannan kuɗi ba. Su ma iyayen nata sun kau da kai daga wani dogon bincike. Ita kuma tana barin gida sai ta tafi wata maciya wadda a da ba

ta zuwa, ta sami wasu daga cikin ƙawayenta na gida, kai har da Magaji da wata ƙawarta da suka yi karatu tare, wato Indo.

**Fitowa ta 2: Lami da Magaji da abokansu a wata maciya**

**Lami:** Kai, ba inda ya fi gida daɗi! Na yi farin ciki da ganin kun sami halarta cikin ƙanƙanin lokacin haka.

**Indo:** Hakan ya yiwu ne da taimakon *Facebook*.

**Magaji:** Haka ne, ai abin ya ba kowa mamaki! Na ɗauka da wasa kike da na ga sanarwarki: "Na zo hutu na sati ɗaya. Mu haɗu yau da daddare !" Na ɗauka ni ya kamata na fara sani in za ki zo.

**Indo:** Kai Lami, amma fa kin… kin yi wani fes da ke. Ban san mene ne a Turai ɗin nan ba, amma duk wanda ya je sai ka ga ya ƙara kyau, da annuri, da lafiya.

**Magaji:** Kada kuma ki manta: ya kuma ƙara kuɗancewa.

**Lami:** E to, me ma zan ce ne? Ina jin daɗin rayuwa a can, ina kuma yin karatun da nake sha'awa, sannan ina samun kuɗi a aikin da nake yi na wucin gadi. Wato a taƙaice dai, ina more rayuwata! Kowa ya ci ya sha abin da yake so, ni zan biya.

**Indo:** Kai Lami, zan bi ki can ni ma! Ba mamaki ki taimaka min na sami gidan aiki ko da na rainon yara ne, ko kuma na samu makaranta ta shirin nan na musayar guraban karatun ɗalibai.

**Lami:** Indo ke nan, wannan ai ba abu ne mai sauƙi ba fa, kin san akwai maganar biza da sauransu.

**Magaji:** Amma ai ke kin haye duk waɗannan! Kuma a gaskiya ban taɓa tsammanin za ki iya dawowa gida hutu da wuri ba. A ce har kin tara kuɗin jirgi? Sai dai in wani ne ya biya miki.

**Indo:** Mhm… Anya kuwa ba kishi kake yi ba, Magaji?

**Magaji:** Kishi? Ni? Sam! Ba wani abu da zai sa na nuna kishi, ko kuwa? Ba shakka ina son Lami, kuma zan iya yin komai don na same ta, ko da ma ta kama na bar ƙasar nan ne.

**Lami:** Da gaske kake za ka yi duk waɗannan saboda ni? Amma zan yi farin ciki idan ka yi hakan. A ce ga ni ga ka a Turai, ai da ba haka ba.

**Indo:** Kun ga ya isa haka – mun zo *party* ne ba wai mun zo nan don tsara rayuwarmu ba! Duk kowa da kowa ya taso mu yi rawa!

**Mai ba da labari:**

Yayin da Lami da abokan arziƙinta suka wayi gari suna tiƙar rawa, suna kuma shaye-shayensu a aljihunta, can kuma a Afirka ta Arewa, ga Faisal can ya yanke shawara. Shi da 'yan wasu mutane masu gudun hijira sun biya wani ɗan fasa-ƙwaurin mutane ya haye da su zuwa Turai. Ga su can ma igiyar ruwa na wuju-wuji da su a tekun *Mediterranean*. Suna ta faman addu'ar kada Allah Ya sa Jami'an Tsaron Kan Iyakar Tekun Turai su kama jirginsu, su dawo da su. Sai dai wani babban abin mamaki yana dab da faɗa musu. Abin da ba su sani ba shi ne, wannan karon abin ya fi ƙarfin tunaninsu. Ku ci gaba da sauraro.

**Fitowa ta 3: Faisal yana ƙoƙarin shiga Turai ta ɓaraunizar hanya**

**Ɗan fasa-ƙwauri:** A saurara, a saurara! Jama'a, na yi iyakar ƙokarina don mu kauce wa Jami'an Tsaron Kan Iyaka. Yanzu mun shiga cikin tekun Turai, saura 'yan kilomita kaɗan mu kai gaɓa. Don haka, ba zan iya wuce nan ba. Daga nan kuma, dabara ta rage ga mai shiga rijiya. Ga alamar gaɓar can kuna hangowa. Abin da za ku yi shi ne ku faɗa ku yi iyo har kun kai gaɓa, in kuma kun ƙi, su kama ku.

**Faisal:** Gaskiya, ba za ta saɓu ba! Mun biya ka a kan za ka kai mu har inda za mu je, ba kawai ka zubar da mu duk inda kake so ba!

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Maza kowa ya kama gabansa! Kada mu tsaya ɓata lokaci. In suka kama mu a nan, to fa mayar da mu Afirka za su yi. Ku tuna fa: Kada ku faɗa musu daga inda kuka fito, sai dai in ƙasarku yaƙi ake yi. Ni zan koma! Ya rage naku, ko dai ku tsunduma cikin ruwa ku yi iyo, ko ku biyo ni zuwa Afirka.

**Faisal:** Allah Ka cece ni!...

**Mai ba da labari:**

Faisal ya dai sami kansa a wani halin neman tsira daga igiyar ruwa mai ƙarfi, da take neman mayar da shi cikin teku. Ba abin da yake ji kewaye da shi sai koke-koken 'yan'uwansa 'yan gudun hijira, kowa yana ƙoƙarin ceton ransa. Ba ya tunanin komai illa ya yi ta iyo har sai da ya kai ga tudun mun tsira. Faisal dai ya ci gaba da iyo har kimanin awa biyu wanda bai taɓa tsammanin zai iya haka ba. Duk da haka gaɓar kamar nisa take ƙara yi masa. Karfinsa na gab da ƙarewa sai ya ji sautin injin wani kwale-kwale yana ƙaratowa kusa da

shi, sai kuma ya ji wata murya mai magana irin ta Turawa tana cewa …

**Jami'in tsaron kan iyakar teku:** Ungo rigar iyo! Kai karɓi rigar iyon mana! … Yauwa, jawo shi! Jawo shi cikin jirgin mana.

**Faisal:** Ku… ku su waye?

**Jami'in tsaro:** Yauwa. Mu jami'an kula da tsaron gaɓar tekun Turai ne. Ka shigo wannan tekun ne ta ɓarauniyar hanya. Waye kai? Daga ina ka fito? Daga Afirka ka fito ko Asiya ko Gabas ta Tsakiya. Ka yi min kama da Larabawa, ko ba haka ba? … Akwai wasu da kuke tare da su a cikin teku?

**Faisal:** Umhh. Umhh. Umhh.

**Jami'in tsaro:** Akwai wasu a cikin ruwan! Tabbas, akwai wasu. Mu ci gaba da tafiya mana! Maza, ba lokaci!

**Mai gabatarwa:**

Daga ƙarshe dai haƙar Faisal ya cimma ruwa. Ga shi ya yi jagab, ga sanyi, ga yunwa, ga kuma ƙishirwa, sannan ga gajiya, amma dai ya kutsa Turai. To, ko me yake jiransa a can? Kuma yaya iyaye da abokan arzikin Lami za su ɗauki wannan ziyara ta Lami zuwa gida? Ku biyo mu zuwa kashi na gaba don ku ji waɗannan bayanan.

Idan kuma kuna son sake sauraron wannan shirin, to ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Allah Ya sada mu da alheri.